SEBHA UNIVERSITY JOURNAL OF HUMAN SCIENCES VOL.23 NO. 1 2024
DOI: 10.51984/JOHS.v23I1.2859

مجلة جامعة سبها للعلوم الإنسانية
Sebha University Journal of Human Sciences

Journal homepage: https://sebhau.edu.ly/journal/johs

# KWATANTA BIKIN SALLAR ASHURA DA YA SHAFI ADDINI TSAKANIN BIRNIN GHAT DA MURZUK

Hassan Mahadi Jibrel

Department of Languages and African Studies, Faculty of Languages, Sebha University, Libya.

**Kalmomin buxewa:**
Bukin cika
Ciki
Ashura
Wasa
Dare
Salla
Addini

**TSAKURE**

Wannan takarda ta na, qoqari bayyana waxansu bukukuwa da suka shafi addini a birnin Ghat da kuma birnin Murzuk,a qasar Libiya.ta hanyar bayani da kwatanta wxannan bukukuwa Wanda Hausawa suke kira da sallar bukin cika-ciki,da kuma Larabawan Ghat da kuma Murzuk suke kira da sunan sallar bukin Ashura.Wanda ake gudanar da shi a ranar tara da goma ga watan Muharam,wato a farkon wata a shekarar musulunci.A garin Ghat a na kiransa da yaren A bzinawa da (Tallitin sibaibai)wato watan Muharam wanda ya zama wani bangare ne na ala'dunsu wadanda suke kiyyewa har ila you . waxannan bukukuwa da ake yi a birnin Ghat suna da siffofi daban –daban.kamar yadda muka ga abaya.wasu daga cikin su suna da halin bakin ciki na kisan Husaini wanda suke kira a Ghat da daren (alali yauxa) wato ita ma kalman abzananci ne ta ke nufin (faduwan sharifi) Awannan takarda an yi amfani da ra'in Edward (1959).domin nazarin qwatanta al'adu.Takarda ta mayar da hankali wajen gano al'adun da suka yi kama da waxanda suka banmbanta,a bangaren Ashura (cika ciki) tsakanin Larabawan Libiya mazaunan garen Ghat da kuma mazauna garen Murzuk.Ta hanyar tattaunawa da hira da kuma ziyartar gani da Ido don yin cikakken bayyani game da bincike.

# مقارنة الإحتفالات الدينية(عاشوراء)بين مدينة غات ومدينة مرزق

حسن مهدي جبريل

قسم اللغات والدراسات الإفريقية، كلية اللغات، جامعة سبها، ليبيا

**الكلمات المفتاحية:**
عاشوراء
عاشوراء
اللعب
الليل
العيد
الدين

**الملخص**

هذه الورقة هي محاولة لشرح الأعياد المتعلقة، بالدين الإسلامي والمصاحبة مع بعض عادات المجتمع، في مدينة غات، ومرزق مع عقد مقارنة، فيما بينهما في كيفية اجراء هذه الأعياد، المتمثلة في عيد عاشوراء الذي يقام في بوم التاسع والعاشر من شهر المحرم، أي في اول الشهر من السنة الإسلامية. وهو عيد يصمه المسلمون، تيمنا بسنة النبي (صلى الله عليه وسلم). لنجاة سيدنا موسى وقومه من بطش فرعون. وفي مديمة غات تسمى بلغة الطوارق (تاليت السبيباي) أي شهر محرم، حيث أضحت جزاء من عاداتهم وتقاليدهم التي يحافظون عليها حتى يومنا هذا.وتسمى ليلة عاشوراء في مدينة غات بأسماء مختلفة منها، احتفالات (سبيباي) وهي كلمة تارقية ويعني بها شهر المحرم. وهذه الاحتفالات في مدينة غات تتخذ اشكالا مختلفة كما سبق وان ذكرنا. ومنها ما يحمل طابع الحزن لمقتل سيدنا الحسين (في موقعة كربلا)ويسمونها أيضا ليلة (ايلالي يوضا) وهي كلمة تارقية وتعني (سقوط الشريف) أي الحسين بن علي ,هذا وقد اعتمدت هذه الورقة علي طريقة المنهج المقارن في دراسة الظاهرة موضوع الدراسة من حيث ابرار أوجه الشبه والاختلاف فيما بين مدينتي غات ومرزق وقد اعتمدت الورقة علي مجموعة من الخطوات من اجل الوصول الي الحقيقة العلمية المتعلقة بموضوع الدراسة نحو الزيارة وحضور هذه الاحتفالات والمشاهدة واجراء لقاءت مع الناس للوصول الي نتائج متمرة .

## 1. Introduction

The 1.0. Gabatarwa:-

Buki wani al'amari ne na farin ciki. Kamar yadda masana suka bayyana, buki al'ada Ce da kowace al'umma ta duniya ke yi a wasu lokuta Na musamman. Ko da yake dai akan sami bambancin yanayin gudanarwa tsakanin wannan al'umma da kuma waccan, to amma akasari an fi tarayya bisa manufar nuna farin ciki kan faruwar wani muhimmin al'amari da ya sami wani ko wasu a cikin al'umma Bukin cika-ciki, ko bukin A shura, buki ne da ya shafi addinin musulunci.

*Corresponding author:
E-mail addresses: has.jibrel@sebhau.edu.ly

*Article History : Received 30 November 2023 - Received in revised form 15 January 2024 - Accepted 16 January 2024*

Hausawa suna kiran wannan buki da bukin sallar cika-ciki.Larabawa kuma suna kiran sa da bukin A shura. Amma wannan salla ba kamar sallar idi ba ce. Ana yin wannan buki ne a ranar tara da goma ga watan Muharram, wato farkon wata a shekarar musulunci. Shi kansa watan Hausawa suna kirnsa da watan cika-ciki. Waxannan ranakun guda biyu, ranaku ne masu daraja da girma da falala a cikin addinin musulunci. Shi ya sa aka yi wa musulmi umarni da su aikata ayyuka na alheri a waxannan ranakun. Musmman azumi da sauran nau'o'in ibada masu qara kusan ta bawa zuwa ga Mahaliccinsa. To amma maimakon waxancan abubuwa da musulunci ya yi umarni da su, sai Larabawa suka qara shigo da wasu abubuwa cikin harkar har abin ya zamo buki. Kusan ma abin da musuluncin ya fi so a waxannan ranaku an bar su kama wasu. A sakamakon haka ma sai suka shigar da wasu camfe-camfe da dama. Waxanda a wurin su za su qara wa ranar girma da daraja a idon al'ummar Larabawa. Daga cikin camfe-camfen da ake yi a wannan rana akwai:Al-qandula, wasa ne da ake yi bayan sallar magriba zuwa sallar isha. Yara ne za su samo xanyen icen dabino sai su xaure qarshensa da wani tsumma su shafe tsumman da mai, sai su kunna masa wuta, suna zagaya gari tawaga-tawaga, suna yin waqoqi don nuna farin ciki da wannan rana.

Mutanen Murzuq da Ghat na qasar Libya suna da ire-iren bukukuwansu na al'ada kafin zuwan addinin Musulunci, waxanda suka danganci bautar gumaka da tsafe-tsafe. Ko da yake ire-iren waxannan bukukuwa nasu suna da yawa. Haka kuma kowanne vangare da irin nasu abin bauta. Sai dai kowace qabila ko iyali da irin nasu bukin, daidai da yanayin gunkin da suke bauta wa. Amma, dangane da wuri da lokutan yin waxannan bukukuwa a qasar akwai lokuta na musamman da suka fi yin irin waxannan bukukuwa, su ne lokutan cin waxansu kasuwanni. Amma da addinin Musulunci ya zo musu sai suka mai da su cikin bukukuwan Sallolin Idi biyu da Mauludi da kuma na Azumin Tasu'a da na Ashura

Wannan shi ya ja hankalin mai bincike, har yake ganin duk vangarorin Gururuwa biyu suna da yanayi kusan iri xaya. Wato daga addinin gargajiya zuwa na musulunci. Saboda haka, a wannan aiki an zo da kamanci da bambancin yanaye-yanayen gudanar da bukukuwan da suka shafi addini a waxannan garuruwa. Sannan kuma an bibiyi da tasirin wani vangare a kan wani, ganin cewa tarihi ya tabbatar da hulxa tsakanin waxannan vangarori guda biyu. Bugu da kari a bin da ya kara mana karfin giwa wajan yin wannan aiki,shi ne ganin rashin yawan rubuce-rubuce a wannan fage, na al'ada.a bin da yajanyo rashin wadatar manazarta.

**1.2.Me ake nufi da bukukuwa:-**

A bin da aka sani game da bukukuwa a gaba xaya,na addini da wand aba ma na a ddini ba,suna daukar dab'iar zamantakewa ta musamman ga wata,al'uma wata ba wata ba. Ma'ana akwai wasu bukukywa da muke samu a cikin al'uma ba wai kwai al'uma xaya ba.misali:-A addinin musulunci ake samu sallar Edi (karamar salla da babbar salla) za mu iya cewa dukkanin al'ummomin musulunci su na yin su sai dai suna daukar halin zamantakewa.

1.3. Me ake nufi da Ala'da:-

Kamar yadda sunan ya nuna kalma ce da ta samo tushenta daga Larabci. Masana da dama sun yi qoqarin bayyana ma'anar ta cikin harshen Hausa. Ga wasu daga cikin su:

Bunza (2006) ya bayyana al'ada da cewa: "Dukkan rayuwar xan'adam tun daga haihuwarsa har zuwa qabarinsa. A ko'ina mutum ya samu kansa duk wata xabi'a da ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu ko yake rayuwa, ita al'adar da za a yi masa hukunci a kai. Babu wata al'umma da za ta rayu a doron qasa face tana da al'adar da take bi, kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata da ba ita ba".

Haka shi ma Magaji (2002), a nasa bayanin cewa ya yi "Al'ada ita ce hanyoyin da al'umma take bi domin gudanar da rayuwarta. Waxanda suka haxa da abinci da sutura da sauran muhimman abubuwa na wannan al'umma".Haka kuma a wajan masanan ilimin fiqho.Ahmed abu sita(2007;10) ya bayyana ma'anr al'ada da cewa,Abubuwa maimaitatu ba tare da alaqa da tunani ko maimaita abu da dawowansa aiki bayan aiki.

**1.3. Bukin Sallar Cika-Ciki a Garin Murzuq.**

Wannan buki, kamar yadda ake yin sa a birnin Ghat, haka ma ake yin sa a garin Murzuq, sai dai yanayin gudanar da shi ya sha bamban sosai. Da farko dai, a Murzuq ba da Sallar cika-ciki suke kiran sa ba, sai dai kawai su ce bukin ranar Ashura. Wannan rana kamar yadda aka sani tana da mutuqar muhimmanci a cikin addinin Musulunci. Wannan ne ma ya sa kusan ko'ina a duniyar Musulunci za a ga ana yin azumi a wannan rana, amma bayan yin ibadar azumi wasu al'ummomi da dama sun shigar da waxansu bukukuwa da camfe-camfe da suke alaqanta su da ibadar wannan rana. To haka ma abin yake a garin Murzuq.Su kuma ga yadda suke yi:

A ranar Ashura, manya da malamai za su taru ne a masallatai da zawiyoyi su raya wannan dare da ibada, kamar yin zikiri da yabon Annabi har zuwa wayewar gari. Su ma mata manya a gidajensu suna taruwa su dinga yin waqe-waqensu na murna da ganin wannan rana. Kuma sukan zaga gida-gida suna yin waqar tare da wata yarinya a bayansu wadda take xauke da wani mazubi mai suna "qufa" (da aka yi shi da kaba) a kanta. Duk inda suka shiga suna yin wannan waqa sai a dinga zuba wa wannan yarinya qwallon dabino a cikin wannan mazubi har dai lokacin da suka gama wasan. Shi kuwa qwallon dabino idan an gama tara shi, akan je ne a jiqa shi domin ya yi laushi. Inda daga baya za a dake shi, a dinga ba wa dabbobi suna ci. Wannan abinci ne mai matuqar muhimmanci da qara lafiyar dabbobi.Su kuwa yara da matasa suna gabatar da bukin ne ta hanyar yin wasanni masu ban sha'awa a wannan rana. Suna saka suturarsu masu kyau kamar na ranar Salla. Wasannnin da sukan yi a wannan rana suna da yawa, daga ciki akwai: 'Shashibani'. Yadda ake yin wannan wasa, shi ne: za a sami wani daga cikin yaran, za a lulluve masa duk jikinsa da kaba, kuma za a xaura qaho guda biyu a kansa. Shi kuma yana riqe da sanda a hannunsa na dama, su kuma ragowar yaran suna kewaye da shi. Daga nan sai ya fara shiga gida-gida yana rawa yara suna yi masa waqa. Su kuma masu gidan za su ba shi abin sadaka, ko kuxi ko gurasa. Idan ya fito kuma daga wani gida yara za su biyo shi suna tsokana, wasu suna riqe da ashana wai za su kunna masa wuta. Shi kuma yana kai musu duka da wannan sanda domin ya kare kansa daga wutar da suke shirin kunnawa (Munira, 2010:123-124). Kilowni (2006) ya dunqule duk abubuwan da ake yi na bukukuwa a garin Murzuq a ranar Ashura zuwa abubuwa takwas, wasu daga cikinsu wasanni ne kamar:

i- Al-banadiq, wasan da ake kwaikwayon harbi da bindiga. Ana yin bindigar ne da icen zarbar dabino wanda za a sassaqa a bisa siffar bindiga sai yara su rabu vangarori biyu suna yaqar juna, kamar yadda sojoji suke yi.

ii- Al-qandula, wasa ne da ake yi bayan sallar magriba zuwa sallar isha. Yara ne za su samo xanyen icen dabino sai su xaure qarshensa da wani tsumma su shafe tsumman da mai, sai su kunna masa wuta, suna zagaya gari tawaga-tawaga, suna yin waqoqi don nuna farin ciki da wannan rana.

iii- Al-bainuwah, shi kuma wannan 'yan mata ne qanana da matasa suke yin sa. Suna samo ganyen dabino ne su sarrafa shi zuwa kayan adonsu na mata, kamar sarqa da xan kunne da awarwaro da zobe. Suna yin wannan kawai a tsakaninsu domin murna da wannan rana.

iv- Xaqxaqah, shi kuma wannan yara ne suke samo zarbar dabino su tsaga ta daga sama sai su yi mata kunne uku. Na tsakiya zai fi tsayi, na gefe da gefe kuma ba su kai shi ba. Idan suka kaxa shi, zai ba da sauti kamar na tafi da hannu.

Waxannan su ne wasanni, ragowar huxun kuma su ne:

v- Yin ado da tufafi sababbi, musamman waxanda aka yi amfani da su a lokutan Babbar Salla da Qarama.

vi- Ziyartar maqabarta.

vii- Haxuwa domin cin abincin dare.

viii- Yi wa juna barka da shigowar sabuwar shekara ta Musulunci.

Wannan shi ne a yadda ake gudanar da bukukuwan ranar Ashura a garin Murzuq. A nan, za a ga akwai bambance-bambance da dama tsakaninsu da na Ghat, inda mafi yawan abubuwan da ake yi a Ghat na ranar cika-ciki, za a ga sun sha bambam. Su kuma na Murzuq wasanni ne ziryan da ba su alaqanta su da wani abu ba.Abin da ya haxa su shi ne, kusan duk manya na vangarorin biyu suna raya wannan rana ne da yin ibada, musamman ta azumi da yin zikiri da yabon Annabi (S.A.W).. Haka kuma su saka sababbin sutura. Sa'id, M. M (2001)

**Bukin Sallar Cika-Ciki a Garin Ghat:- 1.4.**

kamar yadda ake yin sa a birnin Ghat, Sallar cika –ciki a, haka ma ake yin sa a garin Murzuk, sai dai yanayin gudanar da shi ya bambanta sosai. Sai dai a birnin Ghat ba da Sallar cika-ciki suke kiran sa ba, sai dai kawai su ce bukin ranar **Ashura**. Wannan rana tana da mutuqar muhimmanci a cikin addinin Musulunci.Saboda a wannan rana ne Allaha subahanho wata'la ya cito A nnabi Musa daga natsewa a ruwan tikon Maliya,haka kuma a cikin wannan rana ne ya cito Annabi Yaunusa daga cikin Kifi, Wannan ne ma ya sa kusan ko'ina a duniyar Musulunci za a ga ana yin azumi a wannan rana,sabo da godiya da Allah, amma bayan yin ibadar azumi wasu al'ummomi da dama sun shigar da waxansu bukukuwa da camfe-camfe da suke alaqanta su da ibadar wannan rana. Ire-iren waxannan bukukuwa da camfe-camfe za mu bayyana su a lokacin da ake bayyana yadda ake yin bukin a Murzuk. To haka ma abin yake a birnin Ghat. Su kuma ga yadda suke yi:- A ranar Ashura,wato watar Al-Muharam a watanin larabci wanxa ta yi daidai da watar Cika-ciki a wajan Hausawa.Awanan wata a birnin Ghat,tun daga watar Sllalar laiya a ke fara shiri da watan A shura,inda za a ware Naman da za'a yi mafani da su a darin A shurs.Ga yadda suke godanar da wannan biki kamar haka:-

Da zarin ta tsaya watar Muharam,a ranar farko manya da malamai za su taru ne a masallatai su raya wannan rana,ta hanyar karanta Al qurani mai girma.tare da wa'azi haka kuma a karshrn wata za'a taru a saukar da Alqurani mai girma tare da adu'a.Haka kuma a wani bangari,wajn kabilar makera,sune wanda su ke jagurar wasani da kade kade da raye-raye,a watar A shurs a birnin Ghat,Da zarin wata ta tsaya su za su sanar da cewa wata ta tsaya kuma an fara biki ta hanyar buga Ganga a daren tsayawar wata don kowa ya sani ya shirya,da biki da sha shagali a ranuka ma su zuwa waxanda su ke kai har kwana tara,To,da farko dai da marece ta yi yara ne za su fara wasani na su ta hanyar amfani da itatuwan Tunfafiya su kuna wuta a cikin su,suna bugasu itacan suna yin tartsatsi, yaran suke tsalle suke fadi(Alali yuxa-alali yuxa) Da zarin mutane su gama sallar isha'i,sai kowa ya koma gida inda a wannan dare mutanen Ghat suke taruwa iyalai wuri daya a yi a bin cin dare tare a gidan babarsu ko kakasu,Bayan an gama cin a bin ci ,sai Makira su fara buga ganga mutane sutaru,a wannan dare mu su ganga za su fito da rufin sun a gargajiya,a fara zagaya gari ana buga ganga,ana ta rawa idan a ka iso wajan makabarta sai a tsaya a yi adu'a ,a ci gaba da wasa da rawa a na zagaya gari,A wannan dare kowa ya yi shiga ta gargajiya ya sha rawani.da sanda a hannu,ana cikin wasa har a kai tsakiyar birni .idan a ka kai wurin,a wannan dare idan ka ci karo da a bokin wasanka(xan kawunka) a wurin kana iya msa duka,ba tare da kowace masala.Haka ana ta wasa da rawa har akai A hansawa,(A hansawa wurin aikin makira) shi ke nan sai ka ji sun sake kida an buga kidan da a ke kira (cin da wasa) shi kenan sai a ta yi tsalle a na watsewa.kowa ya koma gida.Da haka ya zama an gama da daren farko.

Sai sauran ranuka da suka yi saura ana godanar da su kamar haka:- Ranuka uku na farkon wata ana gudanar da su kamar haka inda za su taru Makera a cikin shiyarsu da ake kaira da (A hannsawa) su fara buga ganga suna waqe-waqensu suna nuna farn cikinsu da wannan rana.Daga nan kuma sai su fara zage gida-gida su ke Ganga da busa.Kowane kabila ta na da nata kida da waka na musamman da su buga musu,da zarin sun shiga gida sai su yi musu kidan su, su shiga rawa suna likawa juna da masu kida da rawa kudi.Haka za a rika ta yi har a zagayo gidaje duk a waxannan ranuka uku .Sai sauran ranuka bakwai yin da suka yi saura za surinka mutane ne a cikin tsakiyar birni,ko a (Ahannsawa) da rufin su nagargajiya sun sha koliya ana kida ana rawa har agama sati guda.Da haka ake godanar bikin A shura a birnin Ghat .

**1.5.-Abubuwan da ake yi na bukukuwa a garin Ghat a ranar Ashura na wasani wasu daga cikinsu wasanni ne kamar haka:-**:

1. A daren A shura kana iya dukar a bokin wasanka wato,(xan kawunka) ,a cikin dariya da was ba tare da kowace masala.
2. wasa ne da ake yi yara bayan sallar magriba zuwa sallar isha na kuna wuta a itaccen Tunfafiya,su ke bugasu da junansu sunafitar da tartsatsai.
3.Zagaya gari a daren A shura ana buga Busa da Ganga tare da waqoqi da rawa.
4- zagaya gidaje ana busa da Ganga da rawa har tsawan qwana uku.
**5-** Yin ado da tufafi na gargajiya,tare da rawani har kala biyu,wato,Baki da fari.
6- Ziyartar maqabarta a darin A shura.
7- Haxuwa domin cin abincin dare a cikin iyali da yara da kakani da jikoki.
8. Yi wa juna barka da shigowar sabuwar shekara ta Musulunci.

Wannan shi ne a yadda ake gudanar da bukukuwan ranar Ashura a Birni Ghat. A nan, za a ga akwai bambance-bambance da kuma kamanci da ke a kwai tsakaninsu birane guda biyun.

1.4.-Kamacin da ke a kwai tsakanin birnin Murzuk da Ghat ya kasance kamar haka:-

1-wasa ne da ake yi yara bayan sallar magriba zuwa sallar isha.
2- Ziyartar maqabarta.
3- Haxuwa domin cin abincin dare.
4- Yi wa juna barka da shigowar sabuwar shekara ta Musulunci.
5-Zagaya gidaje.
6- Yin ado da tufafi sababbi.
7-Su ke kiransa sallar Ashura.

**1.5.-Bambanci da ke a kwai a tsakanin Murzuk da Ghat:-**

1-Wasan Al-banadiq,
2-Ydda yara su ke godanar da wasansu.
3- Al-bainuwah, yadda su ke sarrafa shi ya zama kayan ado da mata.
4-Wasan Xaqxaqah da su ke yi yara a Murzuk ta sha bambam da yaran birnin Ghat.
5- Amurzuk mata ne su ke yin zagaya.Aghat kuwa maza ne

**1.6. Tasirin Zamani a kan Sallar Cika-ciki a Birnin Murzuq da Ghat.**

A lamarin bukin cika-ciki, an sami sauye-sauye da zamani ya kawo. Mata da suke taruwa a da cikin gida suna yin waqe-waqe, yanzu sun daina. Haka kuma matan da suke zaga gida-gida suna yin waqar tare da wata yarinya a bayansu wadda take xauke da wani mazubi mai suna "qufa" (da ake yi da kaba) a kanta. Duk inda suka shiga suna yin wannan waqa sai a dinga zuba mata qwallon dabino a cikin mazubi har dai lokacin da suka gama wasa. Ita ma wannan al'adar an daina yin ta yanzu. Amma dangane da sauran wasannin yara maza na shashibani yana nan ana yi, sai dai ba kamar da ba.

1.7.Haka ma a Birnin Ghat,za mu ga wasu daga cikin al'adu da aka saba gudanar da su a da,an daina yin su a yan zu,kamar al'adar zagaya gidje ana buga Ganga da busa ana rawa,ana bada da masu ganga kudi an daina yin ta.Hakama al'adar duka da abokin wasanka wato yaro ko 'yarinyar Kawaonka ita ma a yanzu an daina.Amma dangane da al'adar wasanin yara kamar kuna wuta a itacen Tunfafiya su rinka bugasu da juna suna tartsatsai yana nan ana yi, har ila yau.Hakama al'adar zagaya gari ana busa da ganga itama ta na nan a na yi.da dai sauran al'adun da muka riga mu ka ambata. Wannan kuwa ya faru ne saboda sauye-sauyen zamani. Inda a yanzu manya da yara ba sa samun damar fitowa sosai,domin yin gudanar da waxannan al'adu , saboda makarantu da suke yi na zamani da kuma kale-kallen tashoshin talabijin na duniya a gidajensu da kuma bibiyar Intarnet,da wasanin na zamani da manya da yara suke yi gaba xaya, Wanda yake xauke musu hankali daga kula da wasanni na gargajiya.da ma da a binda na faruwa a waje.

**1.8. Jawabin Kammalawa**

Kamar yadda aka gani , birnin Ghat da Murzuq suna gabatar da bukukuwan addinin Musulunci kamar bikin Cika-ciki(Ashura) An bayyana a wannan takarda yadda kowane vangare yake gudanar da nasa bukin, tare da kawo ire-iren al'adun da ake yi a waxannan lokuta. Al'adun sun haxa da karatun littattafan addini, musamman Alqurani mai girma da na yabon Annabi (S.A.W) da sabunta tufafi da abinci da yin sadaka da nishaxantar da juna, kamar wasanni iri-iri daga duk vangarorin guda biyu. Haka kuma an ga bambance-bambancen da ya ke tsakaninsu da.da kuma inda suka sha bambam.kamar yadda muka riga muka baiyyana a gabatarwa.babban maqasudin wannan takarda shi ne gano ire-iren waxannan al'adu,na Addini da suka sadu da nagargajiya.ko da yake akan samu karancin litattafai a da manazarta wannan bangare.

**Manazarta**

**Bunza, B.M. (2006) Gadon fexe al'ada. Lagos: Tiwel Nigerian Limited**

Ibrahim, M. S. (1982) "Dangantakar Al'ada Da Addini: Tasirin Musulunci A Kan Rayuwar Hausawa". Kundin Digiri na Biyu. Kano, Jami'ar Bayero.

Magaji, A. (2002) "Wasu Al'adun Hausawa da Yanaye-Yanayensu a Qasar Katsina". Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Koyar da

Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.
Munirah, A. M (2010) *Al-audha Al-idariyyah Walijtima`iyya Wathaqafiyya fi Madinati Murzuq*. Bengazi:Daral Kutub Al-waxaniyya.
Kilowni, I. M. (2006) "Hukumu Shari'at Al-islamiyya Fil Adatil Ijtima'iyya". Kundin Digiri na Biyu. Sabha, Kulliyat Al'dab, Jami'ah Sabha.
Funtua, A.I da Gusau, S.M (2010) *Al'adu da Xabi'un Hausawa da Fulani*. Kaduna : El-abbas Printers and Media Concepts.
Sa'id, M. M (2001) *Zakirat Qaryah* Bengazi: Dar Al-kutub Al-watniyya. Libiya.
Ahmed abu sitta (2007)Alauruf wa al ada fi rai al foqaha.Al mawasu'a Al fiqihiya.Wizarat Al awaqaf wa al shaun Al islamiya Al Kuwait.

**Waxanda aka yi hira da su da ranar da aka yi hirar**

Alhaji Muuhammad Ahmad Karami (13/10/2022) karfe 5 na yamma a garin Murzuq da ke qasar Libya.
Alhaji Abdulsalam Mahammad Saleh (15/10/2022) karfe 10 na safe a garin Murzuq da ke qasar Libya.
Alhaji Ahamed Mahamoud (12\11\2022) karfe 12 na rana a garin Ghat da ke qasar Libya.
Alhaji Basher Hamouda (22\11\2022) karfe 8 na yamma a garin Ghat da ke qasar Libya.